**Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry**

A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)

**DOI:** https://doi.org/10.65760/kassu.i1.25 **Website:** www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Matsayin Karin Magana Da Kirari A Cikin Waƙoƙin Kassu Zurmi

**Shu'aibu A. Jangebe,**
**Halilu Y. Anka,**
**Saifullahi A. Madawaki**

**ZACAS, Gusau**

**Corresponding Author: Shu'aibu Abdullahi Jangebe** shuaibuabdullahijangebe@gmail.com
+1239123933512

**Tsakure**

*Wannan bincike ya yi tsokaci ne a kan karin magana da kirari a cikin waƙoƙin Kassu Zurmi. Binciken zai kawo ma'anar karin magana da kirari da muhimmancin da kuma tarihin mawaƙin a taƙaice sai kuma yadda mawaƙin ke tsalma karin magana da kirari a cikin waƙoƙinsa. Farfajiyar bincikenmu kuma shi ne, wannan bincike kuma zai taƙaita ne kawai a wasu daga cikin waƙoƙin Kassu Zurmi. Hanyoyin gudanar da wannan bincike shi ne, an yi amfani da wasu wallafaffin littattafai da Muƙalu da tattaunawa da wasu mutane da suka san waƙoƙinsa, tare da saurararon waƙoƙinsa da ke cikin "C.D" da kuma kasusuwa. Sai ra'in bincike. Wannan bincike an ɗora shi ne a kan ra'in Waƙar Baka Bahaushiya (WBB) na Gusau, 2003, 2008, da 2014. Sai kuma sakamakon bincike da kuma naɗewa, da za a yi duk a cikin wannan binciken.*

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa:

Kamar yadda manazarta daban- daban (Umar, 1987), Ibrahim, 1983, Ɗangambo, 1984 suka bayyana, a kan tsara waƙoƙin maza ne don a wasa maza, ma'abuta ayyukan ƙarfi da jaruntaka. Al'amura irin su dambe, kokowa, tauri, farauta, sata, caca, abubuwa ne da ke buƙatarƙarfin- hali da shiri na musamman. Da yake waɗannan sha'anoni ne na sayar da rai, masu yin su suna buƙatar zuga da koɗawa. Al'adar Bahaushe ta gargajiya ta tanadi makaɗa na musamman don wasu irin waɗannan mazaje. Misalan irin waɗannan makaɗa su ne, Mamman Ɗan'anace da Kassu Zurmi, da Gambo mai waƙar ɓarayi.

Haka kuma manazarta sun fito da waɗansu abubuwa da ake ganin sun fi fitowa ɓaro- ɓaro a cikin waƙoƙin maza. Waɗannan abubuwa sun haɗa da zuga da Yabo, da nuna

cewa su Jarumai ne musamman 'yan tauri waɗanda suke ganin suna da maganin ƙarfe, har ma da sauran dukanin makamai, wai ba za su yi komi da su ba. (Ibrahim, 1983).

Wani abu da wataƙila ba a faye damuwa da shi ba, har ma ake wucewa ba a lura da shi a waƙoƙin maza ba shi ne matsayin karin magana da kirari.

Koda yake masana (Ɗangambo, 1984; Umar, 1987; ƊanHausa, 2012; Yunusa, 1989) sun yi rubuce- rubuce a kan karin Magana a matsayin ɓangare na ilimi mai cin gashin kansa, a inda suka kawo abubuwan da ya ƙunsa da irin kashe- kashensa, duk da haka ba a maida hankali sosai ba don a zaƙulo karin magana da mawaƙa suka cusa a waƙoƙinsu na maza ba.

Ganin cewa su mawaƙan maza musamman Kassu Zurmi bai yi niyyar mai da hankalinsa kacokan a kan karin magana ba, amma a kan same su jefi- jefi, sai muka ga ya dace a kira samuwar karin magana a cikin wasu waƙoƙin Kassu Zurmi.

Abin da muka yi niyyar yi shi ne mu bi waƙoƙin Kassu Zurmi don mu zaƙulo karin magana in akwai da kuma kawo muhimmancinta ga adabin Hausa.

## 2.0 Hanyoyin Gudanar da Bincike

Wannan bincike ya yi amfani da hanyoyi guda biyu a wajen gudanar da shi. Hanya ta farko ita ce, ta sauraron waƙoƙin da Kassu Zurmi ya yi daga gidajen rediyo da kuma cikin "Kaset" na "CD" da kuma sauraro a cikin na'ura mai ƙwaƙwalwa. Hanya ta biyu ita ce, ta karantarwa daga cikin rubutattun bayanai ba cikin bugaggun littattafai da ƙasidu da aka buga a cikin mujallu da kuma bayanan da ba a buga nan a cikin takardun da aka gabatar a tarurukan ƙarawa juna sani na Jami'o'i.

## 3.0 Ra'in Bincike

An ɗora wannan takarda a kan ra'in Waƙar Baka Bahaushiya na Gusau (2014). Wannan ra'i ya fi karkata ne wajen bayyana tarihi da asali da salsalar waƙar baka ta Hausa, tare da zurfafa bayani kan turke da ayyana tubalan ginin turken da yanayin sassarkuwar a adabi da al'adu a waƙar baka da yanayin awon baka da adon harshe da kuma aiwatar da harshe (Gusau, 2018).

Kasancewar wannan muƙala an yi nazari ne a kan waƙar baka ta Hausa ta Alhaji Kassu Zurmi da kuma yadda yake. Nazarin salon waƙar baka ta Hausa, kuma yana daga cikin gimshiƙan ra'in waƙar baka Bahaushiya. Binciken da za a ƙalailaice a nan shi ne matsayin karin magana a cikin wasu waƙoƙin Kassu Zurmi. Kuma wannan dalili ne ya sa aka ɗora binciken a kan ra'in waƙar baka Bahaushiya don a samar masa da alƙibla managarciya.

## 4.0 Taƙaitaccen Tarihin Kassu Zurmi

An haifi Kassu a wani gari da ake kira Magarya a ƙauyen Kadawa ta Karamar Hukumar Zurmi da ke cikin Jihar Zamfara, a daidai shekara ta 1923. Sunan mahaifinsa Amadu, sunan kakansa kuwa Malam Gandau Dunfawa. Ana yi masa laƙabi da suna Sarkin Fawa Gandau. Sunan mahaifiyarsa "Hauwa'u", wadda ake yi wa laƙabi da suna "Kande".

Sunan Kassu na yanka shi ne Abubakar. Dalilin yi masa wannan laƙabi na Kassu shi ne, saboda an haife shi ne a ranar da aka kafa kasuwar garinsu, shi yasa aka yi masa wannan laƙabi wato Kassu kalma ce ma'ana wai mai kasuwa. Asalin Kassu an ce Bagobiri ne, saboda kakaninsa ne Gobirawa, sun taso daga ƙasar Gobir suka yaɗa zango a wani gari

da ake kira "Dunfawa" ta ƙaramar Hukumar Zurmi. Daga nan sai kuma suka tashi daga garin "Dunfawa" suka koma garin "Magarya". Daga garin na "Magarya", kuma suka matsa zuwa wani ƙauye da ake kira "Kadawa" watau "Kwata", duk a cikin ƙaramar Hukumar mulki ta Zurmi. Kassu ya nuna haka a cikin wata waƙa inda yake cewa:

"Kadawa garinmu ta".

Wannan ya nuna mana cewa shi mutumin Kadawa ne. Kassu Zurmi bai sami damar yin karatun boko na zamani ba, amma ya taɓa karatun Alƙur'ani da sauran littattafai na Fiƙihu. (Gusau, 2005).

Gado Kassu Zurmi ya gaji kiɗa ne a wajen mahaifinsa ya fara bin mahaifinsa wajen kiɗan farauta tun yana ƙarami. Bayan koyon kiɗan farauta da yake yi daga wajen mahaifinsa, ya taɓa kiɗan noma, amma bai mai da hankalinsa ba sosai akansa ba. Shi dai kiɗan farauta ya gada, ya taras ubansa yana yi, don ya himmatu a kansa, har Allah ya ba shi rabo mai yawa a ciki.

A matsayinsa na makaɗin farauta da 'yan Tauri sai mai gidajensu kawai yake bi idan suna ko biki kama ba, a'a tare da shi ake zuwa dajin farauta duk abin da ake yi na farauta a gabansa, ba mai ba shi labari, ra'ayul aini, ne shi. Shi kansa a wasu ɗiyan waƙoƙinsa ya nuna da shi ake zuwa farauta. Dubi abin da yake cewa:

> "Tahiya makoda ko dajin kuna,
> Kowaj ji 'yan kalangaina na tabi an nan,
> Sai da daɗa ka kai naman daji".
> (Waƙar Garugaru na Magaji). (Gusau, 2005).

Kassu Zurmi yana amfani da kalangu a matsayin abin kiɗansa. Kassu ya yi nau'o'in kaɗe- kaɗe a matsayinsa na masanin kalangu. Daga cikinsu akwai: Kiɗan noma, kiɗan farauta na 'yan Tauri, kiɗan ɓarayi da kiɗan 'yan Caca.

Kassu Zurmi ya yi aure cike da zuriya mai yawa. Allah ya azurta shi da 'ya'ya da yawa. Yana da kimanin ɗiya goma sha biyu, shidda maza, shidda mata. Maza sun haɗa da: Umaru ƙaho, Usman, Sani ɗan Gabci, Muhammadu Na Makka, Malam Aliyu, da Rabi'u. A halin yanzu uku na raye, uku sun rasu. Waɗanda ke raye su ne: Muhammadu NaMakka, Malam Aliyu, da Rabi'u. Waɗanda suka rasu su ne: Umaru ƙaho,, Usman, da Sani ɗan Gabci.

'Ya'yansa mata akwai Manga, Salamatu Raule, Bala mardiyya da kuma Nana Asma'u, wadda ita ce auta cikin 'ya'ya mata biyu sun rasu huɗu na nan raye suna aure a gidajen mazansu. Su ne: Raule da Balaraba, da Mardiyya da Nana Asma'u. (Hira da Jikansa Murtala Usman, 18-12-2024).

Daga cikin manyan 'ya'yansa ne, Umaru ya zama makaɗin Tauri, kusan shi ne mai gadonsa. Amma shi ɗaya ɗan nasa Usman sai ya kama hanyar almajiranci inda ya yi karatun allo da na ilimi. Yanzu haka zauren gidansu ne ya mayar makarantarsa ta allo yana koyar da yara karatun allo.

Kassu Zurmi ya rasu bayan wata rashin lafiya da ya yi har ya kwanta asibitin Gwamnati na Gusau a 1987. Wani kauli kuma an ce a 1980. (Gusau, 2005:229).

## 5.0 Ma'anar Karin Magana da Muhimmancinsa

Manazarta da dama sun tofa albarkacin bakinsu game da karin magana. Tun da farko idan aka lura za a ga cewa kalmomi biyu ne suka haɗu, watau kari da kuma magana. Kalmar kari na nufin kakkaryawa, ita kuma magana na nufin zance na yau da kullum. Abin nufi anan shi ne idan mutum ya kware ga harshe to yana iya lanƙwasa magana ta hanyar da ma'anoni daban- daban. Wannan shi ya sa wani malami ya kira karin magana da cewa:

> "Wato gajeruwar jumla ce da ake faɗa ta ƙunshi ma'anoni
> waɗanda ba kasafai kalmomin da ke cikinta ke nuna su ba".
> (Furnise, 1996).

Wannan ya nuna cewa karin magana gajeruwar jimla ce da ake sakaya ma'ana da ita, wadda idan aka warware ta sai ta bayar da ma'ana mai tsawo, wadda mafi yawa kalmomin da ke cikinta ba su ƙunsa ba, sai dai suna da dangantaka da ita.

Dangane da haka muna iya cewa karin magana na da matuƙar amfani domin ba Bahaushe ne kawai yake amfani ko ya mallaki karin magana ba, har ma da sauran harsuna sukan yi amfani da tasu dabara ta sarrafa magana a cikin hikima ko da yake harsunan mutanen duniya sun bambanta, amma wajen azancin magana suna aiki kusan iri ɗaya, sai dai yadda auke amfani da ita a tsarin karin magana tana canzawa daga wannan harshe zuwa wancan harshe. (Muhammad, 2012:43).

Don haka yana daga cikin muhimmancin karin magana gajera ce magana mai yawa. Ta yiwu akan yi haka ne saboda rashin isasshen lokaci na magana, ko dai yin hakan hannunka mai sanda ne da faɗakarwa. Ko don fito da sakacin abu.

Karin magana mafi yawa kukan- kurciya ne inda yakan sanya magana ta yi armashi da daɗi kama zuba magi a cikin miya.

Sannan aka nuna gwanintar laƙantar harshen mai magana da kuma rashin ƙosawar mai sauraro da gina samuwar waɗannan abubuwa masu zuwa kamar haka: Gargaɗi, Ilimantarwa, Nasiha, wasa ƙwaƙwalwa, Ado ga zance, ko Adana adabin gargajiya.

Waɗannan abubuwa da aka ambata a sama abubuwa ne masu matuƙar muhimmanci a cikin maganganun da ke gudana a tsakanin jama'a. Wannan shi ya sa mawaƙan baka musamman a maza ba a kauce wa yin amfani da karin magana a cikin waƙoƙinsu.

## 5.0 Ma'anar Kirari

Manazarta da dama sun tofa albarkacin bakinsu game da ma'anar kirari. Umar, (1987) ya ce kirari kuma tsararriyar magana ce 'yar doguwa, ta hikima, da a kan shirya. Musamman don kambama mutum ko wani abu. A kullum, kirari yana zuwa ne da sigar siffanta ko kamanta abin da ake yi wa kirarin da wani abu ko mutum mai shahararren ƙarfi, ko alfarma, ko daraja, ko dai wani hali na musamman da ya fifita. Abubuwan siffantawa ko kamantawa wajen kirari sukan haɗa da su Giwa, da Zaki, da ayari, da gobara, da ruwa, da baƙin kumurci, da iyaye ko kakanni (musamman ga sarakuna) da jarumawan yaƙi da sauransu. Abin sha'awa shi ne sau tari mutum yakan shirya wa kansa kirari, ya haɗa kansa da kansa. Daga waɗannan mutane akwai magori da 'yan tauri da 'yan dambe da 'yan farauta.

ƊanHausa, (2012) kirari wasu lafuza ne da a kan yi na hikima da nuna balagar ƙwarewar harshe mai magana, domin mutum ya koɗa wani abu idan har buƙatar hakan

ta taso ko mutum ya koɗa kansa kamar yadda masu hikima kan ce "Ɗanmagori koɗa kanka da kanka".

## 6.0 Karin Magana a Cikin Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi

Kamar yadda bayani ya gabata, karin magana kan tuzgo a cikin wasu waƙoƙin Kassu ta fuskoki daban- daban, mafi yawa a yadda aka saba jin su a cikin maganganu yau da kullum ba. Duk da haka, karin magana kan tsaye bisa ma'anoninsu na asali, sai dai lafuzzan ko tsarin faɗar su, su sauya. Misali a wata waƙa ta Kassu mai suna "Waƙar Ɗan'itte na Gidan Gardayi", an sami karin magana kamar haka:

Jagora: Duniya baka nan ta saba,
: Ɗan masu gari ya tsige,
: Ubangiji raz zan Bawa,
: Yana gidan Makau ya hole".
(Kassu Zurmi: Ɗan'itte)

Baitin sama an ɗauko bayaninsa ne daga karin magana nan da ke cewa:

Duniya rawar 'yan mata,

Na gaba ya koma baya.

Akan yi amfani da wannan marin magana ne idan an ga wani mutum yana riƙe da wani babban muƙami, sai lokaci ya zo aka sauke shi daga wannan muƙamin aka bai wa na ƙasa gare shi. To sai ayi irin wannan karin magana.

A wani misali kuma a cikin wata waƙa Kassu Zurmi na cewa:

Jagora: Kaza mai 'yan ɗiya ke tsoron shaho,
: In don ku Dukki sai ta yi kunya.
(Kassu Zurmi: Ibrahim Twosshi)

Haka wannan karin magana take

"Kaza mai 'ya'ya ke tsoron shaho".

Wannan karin magana na nuna cewa, mutum mai abin faɗi shi yake tsoron mutum mai yawan surutu. Ana amfani da wannan karin magana a sa'in da ake magana a game da mutum wanda yake jin tsoron da mutum wanda ake jin tsoron, da kuma dalilin da ya sa ake jin tsoronsa. Watau a kan abubuwa uku ke nan ake yi zancen. Ga wani misali kuma na wannan karin magana mutum mai laifi, shi yake gudun ɗan sanda maras lafiya, shi yake zuwa asibiti.

A nan an nuna cewa mai abin ɗauka shi ke jin tsoron a ɗauke, amma matcaci me ya aje balle wani ya ɗauka.

A wani misali kuma Kassu ya kawo wata karin magana a cikin wata waƙa inda yake cewa:

Jagora: Ban hana yaro hawan kuka ba,

: Amma ya ɓanta takalmi,

: Don ka ya hawo su katsakke,

(Kassu Zurmi: Jabanda)

Wannan karin magana haka yake, kuma haka ya fito. Ana amfani da wannan karin magana ne idan aka ga yaro yana son ya hwaɗa manya ko babba. Sai a yi amfani da irin wannan karin magana.

Wani misalin karin magana da ake samu a cikin wata waƙa da Kassu Zurmi ya kawo, mai nuna cewa:

"Tsuntsun da ya kira ruwa", to shi hwa ruwan za su ci. Wannan karin magana haka take, kuma haka ake amfani da ita. Misali a cikin waƙar:

Jagora: Tsuntsu yai kira ruwa,
: Sun kai ga kunnuwa nai.
Jagora: Maza- maza luddai,
: Damu ya daɗe ga mai jin yunwa.
(Kassu Zurmi: Mai Shibra)

Wani misali na karin magana da Kassu Zurmi ya kawo a cikin wata waƙar yana cewa:

Jagora: Gaskiya mugunyar magana,

: Ba a son ki sai ke tsuhwa.

(Kassu Zurmi: Jabanda Ɗan daji ta)

Wannan karin magana haka take gaskiya mai ɗaci. Ana amfani da irin wannan karin magana, idan ka faɗi gaskiyar abu amma ba a yarda ba. Sai daga baya idan an gano abin haka yake sai a yarda da shi.

## 6.0 Kirari a Cikin Waƙoƙin Kassu Zurmi

Kirari yana iya zama yabon kai, kamar yadda 'yan tauri, ko 'yan dambe ke yi, ko kuma yabon wani, kamar yadda maroƙa ke yi da sauransu. Makaɗa Kassu Zurmi yana amfani da wannan salo na kirari a cikin waƙoƙinsa misali:

Jagora: Kassu Zurmi na tsere ma maroƙa,
: Ko ɗai karka cire man,
: Da mai bugun hwata da na baki,
: Im hwaɗa maku abin da ni tsere ma maroƙa?
: Kowa nattahi roƙo!
: Sai ya binciko ga mai samu yake sauka,
: Niko in nizzo ga wanda bai samu nika jiɗa,
: Gidan marar hujja nike sabka,
: In na ishe akwai, samu mu ci tare,
: in na isheshi ba samu mu raga mashi,
: In yi hira in samu ga maƙwabta.

Jagora: Roƙo ga wanda ba samu wahala ne,
: Kassu sai ni kaɗai da nis saba da irinsu,
: Ni kam na saba da matcata,
: Na kau gode ma na Jatau,
: Ya isa kau mu kirari,
: In na ƙoshi matcata dai,
: Kassu in kaga na hawo doki ka kasa ke,
: In kaga nai sutura da matcata,

: Ga didanmu na gine da matcata,
: Saboda ku kuma in tahi Arhwa,
: In dawo kuma, in tahi Arhwa.
(Kassu Zurmi: Garba Ɗangido)

Anan in muka duba mawaƙin ne watau Kassu ya ke yi wa kansa kirari. Mun ga cewa Kassu yana koɗa kansa da kansa dangane da mawaƙa cewa shi, shi kaɗai ke roƙon matcaci watau 'yan farauta ko 'yan tauri ko ɓarayi.

A wata waƙa kuma makaɗa Kassu Zurmi ya yi amfani da irin wannan saƙo na kirari, inda yake cewa:

Waƙar: Nomau na Magarya
Jagora: Nomau tushen hwaɗa kare masu gari,
: Torankawan tciya uban mairogo,
: Ko hwatare tai yawa taken zamu ako,
: Nomau ko ba ka jin batun masu gari?

Jagora: Na magaji ƙanƙari ba ka jiƙa,
: Gauɗe ba ka matanki,
: Baba kaɗe ba ka baka,
: Nomau tushe hwaɗa karen masu gari.
(Kassu Zurmi: Nomau na Magarya)

Idan an dubi waɗannan ɗiyan waƙar za a ga cewa Kassu yana koɗa gwarzon nasa watau Nomau, inda yake yi masa kirari da cewa matcaci ne koma busasshe ne a wajen tauri.

A wani misali kuma a cikin wata waƙa da Kassu Zurmi ya kawo kirari in da yake koɗa wani gwarzon nasa yana cewa:

Waƙa: Mani Maƙera.
Jagora: Ya gagari gaba Mani,
: Kai na maƙera gudu sai mata.

Jagora: Barkakka da gaba Mani,
: Taho jikan Zaki bari tsoron arna,
: Hwaɗa ma maƙera ina ban kwana,
: Ban dai rena kiran Mani ba,
: Da niz zo wadda a kai duy yai man,
: Zaman doki da ƙahwahu yai man.
(Kassu Zurmi: Mani Maƙera)

Anan Kassu Zurmi yana koɗa gwarzonsa Mani Maƙerada cewa shi "Zaki" ne kuma ba ya da tsoro har yana yi masa kirari da cewa gudu a wajen fama, ko hwaɗa ko yaƙi, to sai hwa mata, ba dai maza ba.

Wani salon kirarai a cikin waƙar da Kassu Zurmi ya yi wa Bahago Baban Mamman Ɗangehe. Kasuu na cewa:

Waƙar: Bahago
Jagora: Ni nikkaima sale kuka na ɗan Bawa,
: Nicce Bahago an yi man Sarauta,
: Wasa hwa za niyi,
: Yacce tayas ko watan bakwai,

: Shege mi naka za ta ci?
: Nicce bari dai a shekara na Marahwa,
: In anka shekara Wasammu tahi kyau,
: Akai gudum muwa da masu kai abinci baki na Asshi,
: Yad daure anka shekara na Marahwa,
: Nittassai dak kwana nic ce masa hwa za a yi,
: Yac ce dakanta dai ina zuwa,
: Raranar asibit an gamo kwanna sanyi,
: Na shige ɗaka,
: Sai najji sallama giwa ta darkako,
: Na Amadu gogan dare,
: Kana hwasa karnai dugunzuma,
: Ni dai ina ɗaka sai naj ji sallama,
: Giwa ta darkako,
: Jin kau ni kai bicit,
: Jin kai ni kai bicit,
: Kaya ɗai ka jiɗa,
: Jin dai ni kai bitib,
: Jin dai ni kai kitib,
: Nij ji sallama nih hito,
: Niy yi nan haka niy yi tuntuɓe da dila,
: Ta kai zuwa cikina nid dawo,
: Nay yi nan, haka kuma niy yi tuntuɓe da ƙunshi,
: Ya kama nan gatona kuma nid dawo,
: Ni koma gadau- gadau,
: Kuma niy yi tuntuɓe da dila,
: Ta kai zuwa guwawuna,
: Nittsaya tsaka nic ce Bahago mi a kashi- kashi
: Yac ce kawo ruwa musha,
: Shege ka san inda nih hito.

(Kassu Zurmi: Bahago)

A nan mun ga cewa Kassu Zurmi ya koɗa gwarzonsa, inda ya kururuta shi ya tula masa ƙasa har ya sa shi ya je ya kwaso kayan jama'a ya kawo wa Kassu ya aji ye masa.

A wani misali na kirari da zamu gani a cikin wata waƙa wadda Kassu Zurmi ya yi wa Mamman Ɗan Sale. Mawaƙin na cewa:

Jagora: Karamin ɗan duniya ka tonon rairai,
: Mamman ya hwaɗa ma ƙoran mata,
: Sai ƙoƙarin ɓantatat tasoshi,
: Shegen ɓarayi an nan,
: Kangama ba ta zancen suna.

Jagora: Gamshiƙa na Sani in kai ne,
: Inji kuuwa an baizanci,
: Hai! Namiji,
: Muhammadu in ji ka ba bugaje haushi,
: To,
: Mala'ikab bugaje,
: Ɗan Sale ciyyon cikin 'yan banza.

Jagora: Tarago mai jan kaya,
: Jirgin bisa mai wattcela 'uway yoya,
: Kama gaba rigimakka na biyo dab baya,
: Ɗan Sanda.

Jagora: Kai masama kowas sami hwan ɗari ya yi,
: Makka in yaƙ ƙiya su mai sai ga bara,
: Akwai mu da rairai masu mai da mutum baya,
: Dukiyab bahili ta yaɗu,
: Sai masu ci sun kawo.

Jagora: Alanya hwatake na dare,
: Ɗan Sale tayin kura,
: Ta yin kura kare ba ya son goyo nai,
(Kassu Zurmi: Mamman ɗan Sale)

A nan Kassu na yi wa gwarzonsa kirari da cewa shi ɗan Sale gamshiƙa ne, tarago ne jan kaya garai kuma shi jirgin sama ne, kuma rairai ne sannan kuma tayin kura ne shi ɗan Sale. Saboda haka mawaƙin yana koɗa shi ne ta hanyar yi masa kirari.

**Sakamakon Bincike**

A sakamakon bincike da muka yi a wannan muƙalar mun gano cewa Kassu Zurmi yana daga cikin makaɗan Maza. Wato masu yi wa Jarumai kiɗa da waƙa. Kamar 'yan tauri da kuma ɓarayi, domin zuga su da kuma yaba su.

A ci gaba da gudanar da wannan bincike an gano cewa Kassu Zurmi yana da fasaha ta ƙulla ɗiyan waƙa. Kuma mutum ne mai yin amfani da salon karin magana da habaici a cikin wasu waƙoƙinsa.

Dangane da wannan bincike an gano cewa Kassu ya aminta da ya riƙe kiɗan gadon gidansu na 'yan farauta da 'yan tauri watau dai kiɗan matsiyata.

Haka kuma a cikin binciken da aka gudanar an gano cewa Kassu mutumin Magarya ne ta ƙasar Zurmi a Jihar Zamfara. Haka kuma mun gano cewa Kassu Zurmi gadon kiɗa ya yi daga wajen mahaifinsa, watau ba ɗan haye na ba.

A cikin bincikenmu mun gano cewa shi Kassu Zurmi matsayinsa na makaɗin Farauta da 'ya

n tauri, tare da shi ake zuwa dajin farauta, duk abin da ake yi na farauta a gabansa, ba wani mai ba shi labari, ra'ayul aini ne shi. Kamar inda a cikin wasu ɗiyan waƙa ya ke cewa:

Tahiya maƙoɗa ko dajin ƙuna,

Kowajji 'yan kalagaina na tahi an nan.

Har ila yau, a cikin wannan bincike da muka yi mun gano cewa sunan Kassu na yanka shi ne "Abubakar". Kassu laƙani ne da ake yi masa. Saboda an haife shi ne ranar da kasuwar garinsu ke ci.

Haka kuma binciken ya nuna mana cewa Kassu Zurmi shi ke kiɗan kuma shi ke rawarsa, watau shi ke ba da waƙa shi ke amshin waƙar.

**Kammalawa**

A takardar kamar yadda ake gani an yi bayani ne a kan karin magana da kirari cikin wasu waƙoƙin Kassu Zurmi. Daga abin da ya gabata za a lura cewa waƙoƙin Kassu Zurmi cike suke da karin magana da kirari, koda yake ba koyaushe ne jama'a suke lura da haka ba. Watakila saboda waƙoƙi ne masu ƙunshe da waɗansu abubuwan da suka fi karin magana da kirari fitowa a fili, kamar zuga ko kuma yabo ga 'yan farauta, ko kuma kirari ga 'yan tauri da ɓarayi. Ganin cewa karin magana da kirari nau'i ne na adabi da ake amfani da shi a rayuwar yau da kullum, yara da manya, maza da mata suna sarrafa shi a maganganun su na yau da kullum, sai muka ga ai shi ma ya kamata a zaƙulo a ga yadda yake. A wannan nazari mun fito da karin magana da kirari gwargwadon hali daga cikin wasu waƙoƙin Kassu Zurmi daban- daban da irin yadda mawaƙin ya sarrafa su domin su dace da sigar waƙa da kuma isar da saƙo.

**Manazarta**

Ɗan Hausa, M.A. (2012) Hausa mai dubun Hikima, Kano. Untery Research and Publishing Company.
CNHN, (2006) Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero. Zaria, Jami'ar Ahmadu Bello University Press Limited.
Gusau, S.M. (2009) Diwanin Waƙoƙin Baka Zaɓaɓɓun Matanin na Waƙoƙin Baka na Hausa. Kano. Country Research Publishing Limited.
Gusau, S.M. (2005) Makaɗa da Mawaƙan Hausa. Kano Benchmark Limited.
Gusau. S.M. (2005) Mazhabubin Ra'i da Tarke a Adabi da Al'adu na Hausa. Kano, Country Research and Publishing Limited.
Gusau, S.M. (2008) Diwanin Waƙoƙin Baka, Juzu'i na Uku. Matanonin wasu Waƙoƙin Alhaji Dakta Mamman Shata Katsina. Kano, Country Research and Publishing.
Yahaya, A.B. (1997) Turken Nazarin Waƙa. Kaduna Fisbas Media Services.